"Kwanan dakon Rana da yini yafi Al-khairi daga Azumin wata da kuma tsayuwar Sallarsa, kuma idan Mutum ya Mutu (yanayi) za'a rika rubuta masa lada kamar yana yi, kuma ana bashi Arzikinsa, kuma za'a tsareshi ga barin fitina"

An rawaito daga Salman Al-farisi -Allah ya yarda da shi- daga Manzon Allah: "Kwanan dakon Rana da yini yafi Al-khairi daga Azumin wata da kuma tsayuwar Sallarsa, kuma idan Mutum ya Mutu (yanayi) za'a rika rubuta masa lada kamar yana yi, kuma ana bashi Arzikinsa, kuma za'a tsareshi ga barin fitina"
[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Gadin Wuni da dare saboda Allah don kare Musulmai, yafi Al-khairi kan azumin wata, da tsayuwar darensa, kuma idan Mai Jahadi ya Mutu aikin ladansa yana wanzuwa yana ci gaba baya yankwa, kuma za’a rika bashi Arzikin Al-janna, saboda yana raye a wajen Ubangijinsa a Al-janna, kuma yana samun Karama ta yadda Mala’iku biyu basa su masa ba don tamabaya (a Kabari) kuma wancananka saboda ya Mutu ne yana mai dakon kare Addinin Allah Madaukakin Sarki, tare da sanin cewa Mai zaman dako a tafarkin Allah; saboda shi ya lazamci wuraren Iyakoki don kariyar ga Musulmai daga Kafirai

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/2752